Ya Abubakar, me kake zato da mutum biyun da Allah Shi ne na ukunsu

Daga Abubakar al-Siddiƙ - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Na kalli digadigan mushrikai akan kawunanmu alhali mu muna cikin kogo, sai na ce: Ya Manzon Allah da a ce ɗayansu zai kalii digadigansa zai ganmu a ƙarƙashin digadigansa, sai ya ce: «Ya Abubakar, me kake zato da mutum biyun da Allah Shi ne na ukunsu».
[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Sarkin muminai Abubakar al-Siddiƙ - Allah Ya yarda da shi - a lokacin hijira: Na kalli digadigan mushrikai alhali su suna tsaye akan kawunanmu a saman kogon Hira alhali mu muna cikinsa, sai na ce: Ya Manzon Allah da a ce ɗayansu zai yi duba zuwa ga digadigansa zai ganmu ƙarƙashin digadigansa, sai ya ce : Ya Abubakar, me kake zato da mutum biyu Allah ne na ukunsu da nasara da kuma taimako, da kiyayewa da kuma daidaita?!

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/3447